# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na shida: Hangen Dala Ba Shiga Birni Ba


| | |
|---|---|
| Wadda ta rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya fassara: | Ɗanlami Bala Gwammaja |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Faisal: | ɗan shekara 19 |
| Suleman: | ɗan shekara 19 |
| Mai gabatar da labarai: | ’yar shekara 30 |
| Malam Talle: | ɗan shekara 60 |
| Matar M. Talle: | ’yar shekara 55 |
| Lami: | ’yar shekara 20 |
| Magaji: | ɗan shekara 22 |
| Sa’adatu: | ’yar shekara 35 |

**Mai gabatarwa:**
Jama'a, barkanmu da sake saduwa a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" a inda muke gabatar muku da jerin wasan kwaikwayo ta wannan gidan rediyo mai suna "Tudun mun tsira – Mai bayani a kan 'yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai". Shi dai wannan shirin na namu na yau sunansa "Hangen Dala ba shiga birni ba".
Bari mu fara da sauraron Faisal da babban abokinsa Suleman yayin da suke kallon talabijin. Faisal ya ga an nuno shi a labarai, sai ya ga abin kamar a mafarki. Ana ba da labarin wani jirgin ruwan da aka tare, maƙil da 'yan gudun hijira, yayin da suka yi yunƙurin kutsawa Turai. Faisal dai bai taɓa faɗa wa kowa yunƙurin da ya yi a kan hakan ba, har ma shi kansa babban abokin nasa, wato Suleman.

**Fitowa ta 1: Suleman da Faisal suna kallon labarai a talabijin**

**Mai gabatarwa:** Jama'a, barkanmu da saduwa a shirin "Labaran Karshen Mako". Waɗannan 'yan gudun hijirar da muke gani wanda wasunsu sun fito ne tun daga Tsakiyar Afirka, Hukumar Kula da Gaɓar Tekun Turai ce mai suna 'Frontex' ta kama su a ranar Litinin a yayin da suke ƙoƙarin kutsawa Turai ta ruwa. Mun sami labarin cewa akwai wasu da dama da suka rasa rayukansu a hanya saboda ƙishirwa. Ɗaya daga cikinsu kuma ya yi alkafura…

**Suleman:** Kai Faisal, me ya sa ka canza tashar! Wancan mutumin da aka nuno ya yi matuƙar kama da kai. Ko ba ka gan shi ba ne?

**Faisal:** Ka san dai ni ba makaho ba ne, ba kuma kurma ba ne! Na gani.

**Suleman:** Lallai kai ne, ko kuwa? Amma ko ka faɗa min! To yaya ke

nan? Har yanzu kana tunanin shiga Turai ta jirgin ruwa? Ka san fa kama ka za su sake yi su kuma dawo da kai za su yi!

**Faisal:** To, sai me? In za su dawo da ni sau shurin masaƙi, ni ma sai na yi ta komawa har sun gane ni, sun kuma fahinci ba ni da niyyar fasawa. Daga nan sa ƙyale ni na shiga. Ka ga Suleman, haƙanmu ya kusa cimma ruwa! Kada mu ja da baya mutumina.

**Suleman:** Allah ko? To, kuma yaya za ka yi idan ma'aikatan 'Frontex' ba sa kusa a lokacin, ballantana ma za su tsamo ka daga cikin ruwa?

**Faisal:** Sai na yi ta iyo irin wanda ban taɓa irinsa ba. Kai, Turai: Hangen Dala ba shiga birni ba.

**Mai ba da labari:**

Duk da ganin halakar da Faisal ya yi ƙuru-ƙuru, hakan bai sa ya karaya ba. Anya zai iya sake sai da ransa kuwa, ya sake ƙoƙorin kutsawa Turai? Ku biyo mu dai. Amma yanzu, bari mu doshi kudancin nahiyar, don jin abin da iyayen Lami ke cewa yayin da suke hira bayan sun ci abincin dare. Malam Talle ya damu a kan ko wane hali 'yarsa ke ciki game da karatunta a Turai.

**Fitowa ta 2: Mutanen gidan Malam Talle bayan gama cin abincin dare**

**Matar M. Talle:** Kana yawan damun kanka, Maigida. Kada fa abin ya taɓa lafiyarka. Lami ta ce babu abin da yake damunta. Ai wannan ya isa ya kwantar mana da hankali.

**Malam Talle:** A'a, da jin maganarta kin san akwai abin da yake damunta. Na santa sarai. Kuma wace ce wannan ƙawar da ta samu?

Kwananta ɗaya fa tak a wannan nahiya, amma a ce har ta yi ƙawa?

**Matar M. Talle:** Ka fa san Lami yarinya ce mai haba-haba da mutane, ga ta kuma kyakkyawa. Ba wani abin mamaki ba ne in ta yi ƙawaye haka da gaggawa.

**Malam Talle:** Ana ba ki kina ƙin karɓa, yarinyar nan ta je Turai ne don ta yi karatu ba ƙawaye ba. Ai tana da ƙawaye birjik a nan.

**Matar M. Talle:** Kwantar da hankalinka, Maigida. Na fahimce ka. Abin da nake nufi shi ne, ita fa ba yarinya ba ce yanzu, ta mallaki hankalin kanta. Na kuma tabbatar, wallahi ba za ta ba mu kunya ba.

**Malam Talle:** Ni dai ina ji a jikina akwai wani abu. Bai kamata mu tura ta Turai ba. Har yanzu yarinya ce. Kuma har shekara uku!

**Matar M. Talle:** Ka ga ya isa haka. Ka daina yi mata mummunan zato. Ba abin da zai same ta. Ba ta taɓa barin gida ba ko da da rana ɗaya! Ai dole ta ji ba daɗi.

**Malam Talle:** Ai ba zan sami nutsuwa ba sai na sake yin magana da ita. Kin san *network* ɗin ba kyau sanda muka yi magana da ita, kuma ba na jinta sosai.

**Matar M. Talle:** Ina fatan dai ba ka faɗa mata cewa a halin yanzu ba mu da kuɗin da za mu biya mata cikon kuɗin karatunta na shekara biyu ba?

**Malam Talle:** Haba, ina! Don me zan faɗa mata? Amma kin san tana da tunani, ba mamaki ta gano hakan. Za ta san yadda za ta yi ta karasa karatun. Tun da dai ta riga ta fara, ai ba za ta

fasa ba.

**Mai ba da labari:**
Gaskiya ne cewa Lami na jin daɗin karatun da take yi na lauya, amma babarta ta yi kuskure da ta ɗauka cewa ’yarta za ta yi sabo da yanayin Turai cikin gaggawa. Bari mu leƙa wajen Lami a cikin ɗakin cin abincin jami’arsu, mu ji irin hirar da suke yi da saurayinta Magaji ta intanet.

**Fitowa ta 3: Lami da Magaji suna hira ta intanet**

**Magaji:** Yaya kike amaryata?

**Lami:** Lafiya ƙalau angona.

**Magaji:** Ya karatun? Ina fatan dai waɗannan Turawan na kula da ke sosai?

**Lami:** Karatu alhamdu lillahi! Turawa kuma muna zaune lafiya. Yaya kake?

**Magaji:** Ga ni nan dai. Yaya kike yi wajen harkar kuɗi kuwa? Ko kina buƙatar taimako ne? Na san akwai tsadar rayuwa a Turai, musamman ma wajen ɗalibai.

**Lami:** A’a, ba na buƙatar komai. Kai ma nauyi ya riga ya yi maka yawa.

**Magaji:** In dai kina buƙata ki faɗa min kawai! Kin san mahiyar Afirka ma na iya aikawa da taimako zuwa Turai.

**Lami:** Hahaha, ba ka rabo da abin dariya. Zan yanke hirar nan

tamu, ina fatan ba za ka damu ba.

**Magaji:** Kai! Tun yanzu? Ba yadda za a yi na gan ki ta kyamarar intanet? Yau fa wata huɗu ke nan.

**Lami:** Ba zai yiwu ba, wannan kwamfutar ba ta da kyamara. Sai mun yi magana gobe. Ka san ina mutuwar sonka.

**Magaji:** Ni ma haka. Sai mun yi magana.

**Mai ba da labari:**
Lami dai ta fita daga intanet cikin rashin jin daɗi. Dalili kuwa shi ne, wannan shi ne karo na farko da ta yi wa wanda ta ce tana so kuma take so ta aura ƙarya. Maganar gasikya ita ce, da farko dai tana cikin tsananin buƙatar kuɗi, na biyu kuma ba wani abin da za ta yi a wannan lokacin, na uku kuma wannan kwamfutar tana da kyamara. Daga nan sai Lami ta tashi ta nufi gidan waya ta kuma lalubo lambar wayar Sa'adatu.

**Fitowa ta 3: Lami ta kira lambar Sa'adatu ta waya**

**Sa'adatu:** *Hello*? *Hello*, Sa'adatu ce ke magana.

**Lami:** *Hello* Sa'a, Lami ce. Kin tuna da ni ko?

**Sa'adatu:** To! Lami ce. A'a'a, babbar lauya ke nan! Yaya zan manta ki? Yaya kike? Na ji muryar taki kamar ranki a ɓace.

**Lami:** Mhm…ki dai bari kawai. Ta ina ma zan fara ne. Yanzu dai watana huɗu da zuwa Turai don na yi karatu, kuma na koyi abubuwa da yawa, amma… Sa'adatu, rayuwa tana da matuƙar tsada! Ina ganin 'yan'uwana ɗalibai suna fita gari

*weekend* amma ni ina ƙunshe a *hostel* kamar mai gadi. Koyaushe a waje suke cin abinci, amma ni ba ni da ikon yin haka. Suna sa kaya masu kyau, amma ni sai waɗanda na zo da su nake ta sawa, ga shi ma ko wata rigar sanyi ta kirki ba ni da ita.

**Sa'adatu:** Iyayenki ba sa taimaka miki da kuɗin kashewa ne?

**Lami:** Ba sa aiko min da kuɗi. Na san ba su da iko, duk da cewa ba su faɗa min ba. Na san sun yi amfani da duk abin da suka tara wajen turo ni nan na yi karatu. Yanzun nan na yi magana da... da saurayina ta intanet. Ya gaya min ya sami aiki, sai dai ba zan iya tambayarsa kuɗi ba. Ko me kike gani?

**Sa'adatu:** Sam! Kada ki tambaye shi! A fa Afirka yake, Lami. Mutanen da suke can sun fi na nan buƙatar taimako. Ah! Me ya sa na ce kada ki kuskura ki faɗa musu gaskiyar halin da kike ciki?

**Lami:** Kin san mutanenmu ba za su yarda ba. Zai yi wahala su fahimta.

**Sa'adatu:** Yauwa, haka abin yake! Su mutanenmu ba abin da ya sha musu kai da cewa ke ɗaliba ce wadda ba ta da kuɗi, ko ma a titi kike kwana, idan dai kina Turai, to fa kin shigo gari! Kin ga Lami, kada ki damu. Za mu nemi mafita, kin ji. Manta da wannan saurayin naki. Zan ba ki wasu 'yan kuɗi a matsayina na ƙawarki. Ki yi amfani da su ki sayi 'yan riguna masu kyau da kuma kayan kwalliya da sauran wasu 'yan abubuwan dai. Kin ji? Bari mu ga yadda za mu ɓullo wa abin. Yauwa! Ki tuna fa a Turai kike! Nan ne inda kowane ɗan Afirka yake mafarkin zuwa.

**Lami:** Na gode Sa'adatu! Ban san irin godiyar da zan yi miki ba. Wallahi kin kyauta mini! Sai dai na ce Allah Ya bar mu tare. Na gode sosai, Sa'a!

**Sa'adatu:** Ki share kawai Lami. Yauwa, ki kira ni gobe sai mu shirya inda za mu haɗu. Sai mun yi magana!

**Lami:** To Sa'a, sai goben. Na gode.

**Mai gabatarwa:**
Wannan shi ne lokaci na farko da Lami ta yi murmushi tun da ta je Turai. Ba ma alƙawarin taimakon kuɗi Sa'adatu ta yi wa Lami kawai ba, ta ce za su tattauna yadda za ta taimaka mata ta dinga samun ɗan kuɗin shiga. Kowane irin tunani Sa'adatu ɗin take da shi a kan wannan? Kada mu manta, ta faɗa wa Lami ta ma manta da Magaji. Shin ko Lami za ta karɓi wannan shawarar? Za mu ji waɗannan bayanai nan gaba don kuwa mun zo ƙarshen wannan shirin na yau wanda shi ne kashi na shida a cikin jerin wasan kwaikwayonmu na wannan gidan rediyon mai bayani a kan gudun hijira daga Afirka zuwa Turai.
Muna maraba da ra'ayoyinku, da shawarwarinku a kan gudun hijira ba bisa ƙa'ida ba ta ruwa. Kwa iya yin hakan ta shafinmu na Facebook, wato facebook.com/dw.lbe. Ku huta lafiya.